JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 12 Muharram, 1443

MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 20 Ogusta, 2021

(1)

## YAYE DAMUWA DA TASIRINSA AKAN MUTANE A MATSAYINSU NA ƊAIƊAIKU DA NA AL'UMMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku aikata alhairi saboda ku sami babban rabo)** [al- Hajji: 77], haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Magana mai daɗi, gami da yafiya sun fi sadakar da aka bibiye ta da cutarwa alhairi, lallai Allah mawadaci ne mai kuma yawan huƙuri)** [al-Baƙra: 263]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya, ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabin mu Muhammad bawansa ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci ya zo da saƙon da yake tattare da ɗaukacin kyawawan ɗabi'u, da ƙololuwar abin koyi, a cikin waɗannan kyawawan ɗabi'u akwai: ɗabi'ar yaye damuwa, ɗabi'a ce da take nuna darajar ran mai ita, da kuma sauƙin kansa, lallai Allah mai girma da buwaya ya girmama sha'anin wannan ɗabi'a mai daraja, inda ya sanya ta zama ɗaya daga cikin sifofinsa, wadda ta ratayu da sunansa ***"al- Jabbaru"***, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Shi ne Allah wanda babu abin bauta wa da gaskiya sai shi, ainihin mamallakin komai, cikakken da babu wata tawaya tare da shi, kuɓutacce ga barin abin da bai dace da**

**shi ba, amintacce ga barin naƙasa, wanda ya gasgata manzanninsa ta hanyar ƙarfafa su da mu'ujizozi, mai lura da komai, mai rinjayen da babu abin zai gajiyar da shi, mai babban sha'ani a ƙarfi da iko wajen yaye damuwa..)** [al- Hashr: 23], yana yaye talauci da wadata, yana yaye cuta da lafiya, yana yaye tsoro gami da baƙin ciki da natsuwa, a cikin ma'anonin wannan suna –kaman yanda Imam al-Ƙurɗabiy (Allah ya ƙara yi masa rahama) ya faɗi- akwai mubalaga wajen yaye damuwa, kalmar ta samo asali ne daga ma'anarta na fi'ili *"jabara"*, watau: idan ya gyara abin da ya karye, ko ya wadata talaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan yi addu'a ya ce: **(Ya Allah ka gafarta mini, ka yi mini rahama, ka shiryatar da ni, ka yaye mini damuwa, ka azurta ni).**

Haka ma Allah Maɗaukakin Sarki ya bayyana wa bayinsa, ta hanyar yaye masu damuwarsu, da sanya su cikin jin daɗi, ga mahaifiyar Annabi Musa (AlaiHis Salam) nan, a lokacin da zuciyarta take tafarfasa akan ɗanta, tana tsoron kada wani abu mai muni ya same shi, sai kuwa Allah ya dawo mata da shi; saboda ya yaye mata wannan damuwa gami da alhini da ta shiga, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Sai muka dawo da shi zuwa ga mahaifiyarsa; saboda ta sami natsuwa, kada ta cigaba da damuwa da baƙin ciki, saboda kuma ta san cewa lallai alƙawarin Allah gaskiya ne; sai dai mafi yawan su ba su san haka ba)** [al-Ƙasasi: 13]. Lokacin da Annabimu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya fita daga ƙasarsa Makka, Allah ya yaye

masa damuwa, inda akan hanyarsa ta zuwa garin Madina ne ya yi masa wahayi yana ce masa: **(Lallai wanda ya saukar maka da Alƙur'ani mai girma, tabbas zai sake dawo da kai zuwa ga garinka)** [al- Ƙasasi: 85], ma'ana: zai sake dawo da kai zuwa garin Makka.

Haka ma ɗabi'ar yaye damuwa ta bayyana a cikin rayuwar Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), lokacin da ya dawo gida wurin matarsa Sayyida Khadija (Allah ya ƙara yarda da ita), yana zaton cewa wani abu na sharri ya kama shi, cikin sauri ta kwantar masa da hankali, ta yaye masa damuwa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ta ce masa: **"Ina, wallahi har abada Allah ba zai tozartar da kai ba; saboda tabbas kana sada zumunci, kana ɗaukan nauyin marasa shi, kana bayar da taimako ga waɗanda suke cikin talauci, kana shirya wa baƙi liyafa, kana taimakon wanda ya shiga cikin matsin rayuwa"**. Haka ma lokacin da Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya haɗu da Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da shi) cikin wani yanayi na damuwa da karaya, sakamakon shahadar da mahaifinsa Sayyiduna Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da shi) ya yi, ya bar masa iyalai da kuma bashi, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yaye wa Sayyiduna Jabir (Allah ya ƙara yarda da shi) wannan damuwa, ya ce masa: **(Shin ba na yi maka albishir da abin da Allah ya tarbi babanka da shi ba?... Allah bai taɓa yin magana da wani halitta ba sai ta bayan hijabi, amma mahaifinka Allah ya raya shi ya yi magana**

**da shi ba tare da hijabi ba, sai ya ce masa: Ya bawa na, ka faɗi abin da kake son in ba ka, sai ya ce: Ya Ubangiji, ina son ka sake raya ni, a kashe ni saboda kai, sai Ubangiji mai girma da buwaya ya ce: Ai tuni na riga na tabbatar da cewa ba za su sake dawowa zuwa duniya ba)**.

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya buga babban misali wajen yaye damuwa, lokacin da talakawan mutanen Makka *"al-Muhajirun"* suka zo wurinsa suka ce: ya Manzon Allah, masu hannu da shuni sun kwashe lada, suna yin Sallah kamar yadda muke yi, suna kuma yin Azumi kamar yadda muke yi, suna kuma yin sadaka da abin da ya yi saura cikin dukiyarsu. Ya ce: **(Shin ashe Allah bai ba ku abubuwan da za ku yi sadaka da su ba? Lallai duk tasbihin da za ku yi, kuna da ladan sadaka, haka ma duk kabbarar da za ku yi, kuna da ladan sadaka, duk godiyar da za ku yi, kuna da ladan sadaka, duk hailalar da za ku yi kuna da ladan sadaka, umurni da aikata alhairi sadaka ne, hana mummunan aiki sadaka ne..).**

Duk wanda ya lura da Shari'ar Musulunci da kyau, zai ga cewa lallai ta zo ne domin ta yaye damuwa ɗaukacin mutane, musamman masu rauni daga cikinsu, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ka ga kada ka zalunci maraya, haka ma kada ka hantari mai bara)** [ad- Dhuha: 9 - 10], ma'ana ka yaye masu damuwa, ka kyautata masu. Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Shin ma wai ana taimakonku, a kuma azurta ku ne ba domin masu raunin cikinku ba?!)**, haka ma (SallalLahu

alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ni da mai rainon maraya a cikin gidan aljanna kaman haka muke –ya yi nuni zuwa ga manuniyar yatsarsa da ta tsakiya)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya tsaya wa bazawara, da miskini, daidai yake da wanda ya yi jahadi fisabililLahi, ko wanda ya yi tsayuwar dare, ya kuma yi azumi da rana)**, lokacin da aka tambayi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) aka ce: wane aiki ne ya fi falala? Sai ya ce: **(Ka shigar da farin ciki a cikin zuciyar ɗan uwanka Musulmi, ko ka biya masa bashi, ko ka ciyar da shi abinci)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Mutumin da Allah ya fi so shi ne wanda ya fi amfanar mutane, ko aikin da Allah ya fi so shi ne farin cikin da ka shigar a cikin zuciyar Musulmi, ko ka yaye masa damuwa, ko ka biya masa bashin da ake binsa, ko ka fatattaki yunwar da take damunsa, wallahi na fi son in tafi tare da ɗan uwa na in biya masa buƙatarsa, akan in yi ittikafi na wata ɗaya a wannan Masallaci, cikin Masallacin Madina)**.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Babu shakka kan cewa lallai ɗabi'ar yaye damuwa ɗabi'a ce mai girma, wadda ta faɗaɗa ta game da taimakekeniya tsakanin al'umma a rayuwarsu ta zamantakewa, shi addinin Musulunci bai san wani abu wai shi son- kai, da nuna halin ko in kula ba, abin da addini ya sani shi ne: taimakekeniya cikin gaskiya, da lura da zukatan mutane, da yaye masu damuwa, domin Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar juna, da tausayin juna, da nuna damuwa da juna, kaman gangan jiki ne guda ɗaya; wanda idan wata gaɓa daga ciki ta sami matsala, take sauran jikin yake kamuwa da rashin barci da zazzaɓi)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda yake da abin hawa sama da buƙatarsa, to ya bai wa wanda ba shi da abin hawa, duk wanda yake da guzuri sama da buƙatarsa, to ya bai wa wanda ba shi da guzuri)**.

A nan lallai muna son mu ƙara tabbatar da cewa shi yaye damuwa kaman yanda yake kasancewa ta hanyar aiki, haka ma zai iya kasancewa da magana mai kyau, ko ta hanyar addu'a ta gaskiya, ko ta hanyar yin nasiha saboda Allah, ko ta hanyar yin murmushi mai sanya farin ciki, saboda Annabimu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Kada ka kuskura ka raina aikin alhairi, kai koda ka haɗu da ɗan uwanka ne da sakakkiyar fuska..)** ma'ana: kana masa murmushi mai sanya farin ciki, haka ma muna ƙara tabbatar da cewa ita ɗabi'ar yaye damuwa tana da tasiri mai

girma wajen sanya soyayya a cikin zukata, da haɗa kai tsakanin al’umma.

**Ya Allah Ubangiji ka azurta mu da aikata ayyukan alhairi, da yaye damuwar bayin Allah.**